**Competitive Scramble is an Evil Ingenuity: Proceedings from the International Conference on the Biography and Songs of Alhaji Abubakar Kassu Zurmi in Heroic Poetry**

A Publication of the Department of Nigerian Languages, Sokoto State University, Sokoto



| ISBN 978-978-62480-5-9 (Print) | ISBN 978-978-62480-5-9 (Online)

**DOI:** https://doi.org/10.65760/kassu.i1.26 **Website:** www.ssu.edu.ng |**Issue 1 | April 2025**|

# Mazan Kashin Maza, Maza Ke Tsoro: Kassu Zurmi Jagoran Faɗa Da 'Yan Ta'adda

**Yakubu Aliyu Gobir**

Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu Danfodiyo, Sokoto

**Corresponding Author:** Yakubu Aliyu Gobir aliyu.gobir@udusok.edu.ng
08035605024

**Tsakure**

*Manufar wannan maƙalar shi ne fito da gudummuwar waƙoƙin Kassu Zurmi wajen samar da tsaro. Maza su ke samar da tsaro kuma su ke wargaza shi. An saurari waƙoƙin Kassu Zurmi da aka taskace cikin wasu ayyuka da kuma tattunawa da masana da manazarta, domin samo bakin zaren matsalar tsaro, kamar yadda Kassu Zurmi ya fito da su. Aikin ya gano cewa, tsaro ba ya samuwa a cikin al'umma har sai mahukunta sun yi aikinsu, su kuma jama'a sun taimaka musu. Barin jama'a suna ɗaukar mataki/doka a hannunsu ba shi ne mafita ba.*

**Copyright:** *Provided that the author(s) and the source are credited, noncommercial use of the article is allowed, including printing and distribution.*

## 1.0 Gabatarwa

Waƙoƙin Baka wani rukuni ne na adabi wanda ke ƙunshe da saƙonni daban-daban, musamman waɗanda suka shafi hannunka mai sanda, a kan faɗakarwa ko gargaɗi ko kuma abin da Hausawa ke cewa: 'Hankali da kaya, ya fi ban cigiyya'. Masana da manazarta irin su Gusau (2008 da 2011 da 2023) da Magaji ( 1980) da Yahya (1997) da Bunza (2009 da 2014) da Funtua (2015) da Kaura (2017), da sauransu, sun yi rubuce-rubuce a kan waƙoƙin Hausa da rabe-rabensu. Daga cikin rabe-raben waƙoƙin baka akwai na maza, wato waƙoƙin jarumta, waɗanda ke zaburar da jama'a ma'abuta jarumtaka, domin nuna bajinta musamman a wajen tsaron rayukkan jama'a da dukiyoyinsu. Manufar wannan muƙalar shi ne fito da gudummuwar da Makaɗa Kassu Zurmi da taurarinsa suka bayar wajen samar da tsaro a yankin Zamfara da Gobir.

## 1.1 Fashin Baƙin Fitullun Taken Maƙala

Na yi wa wannan maƙala taken: "Mazan Kashin Maza, Maza Ke Tsoro: Kassu Zurmi Jagoran Yaƙi da 'Yan Ta'adda", dalilin wannan taken shi ne, kowace al'umma ta duniya, ta farar fata da baƙar fata, tsaro shi ke kafa ta. Kuma ga tsarin dokokin duniya, har na zamani na UN, maza ke gaban tsaro. Maza sun fi yawa ga soja, sun fi yawa ga ɗansanda, sun fi yawa ga Jami'an Tsaro na Farin Kaya (D.S.S.) da sauransu, kuma wannan ya haɗe duniya gaba ɗaya. Hatta da Ingila da Amerika da Canada, da Jamus, a wajen yawan masu tsaro, maza sun ninka mata sau 3, a wasu ƙasashen ma sun ninka su sau 5. Don haka, Kassu Zurmi ya fahimci, abin da a tsaro shi ne "Namiji". abin da ke ɓata tsaro shi ne "Namiji". Kassu, ya yarda da maza ke noma maza ke farauta kuma su ke kawo abin da za a ci, don haka ya yi musu waƙoƙi da kansa. Ya kuma fahimci ga sata, maza ke kan gaba, domin ga ƙa'idar waƙoƙinsa, babu inda ya ambaci "mace" ɓarauniya. Mutum guda ya ambaci mace ɓarauniya shi ne Gambo. Amma duk waƙoƙin Kassu, babu inda ya ambaci "mace" ɓarauniya.

## 1.2 Dubarun Bincike

An yi ƙoƙarin bin hanyoyi daban-daban, domin tattara bayanan da aka yi amfani da su wajen haɗa wannan muƙala. Hanyoyin sun haɗa da:

1. Sauraron Waƙoƙin Kassu Zurmi a MP3, da kuma waɗanda aka taskace a rubuce da wasu masana suka yi a cikin wasu ayyukan bincike.
2. Tattaunawa da sauran jama'a masu hannu da tsaki a kan harkar tsaro musamman a Zamfara da yankin Gobir, da ma'aikatan tsaro, da 'yan sa-kai,
3. Ziyartar ɗakunan karatun hukuma da Jami'o'i, da manyan makarantu, domin samo ayyukan da masana, da ƙwararru, suka yi a kan bagiren da nake bincike.
4. An yi ƙoƙarin kasa kunne, da zura ido, ga rahotannin kafafen yaɗa labarai, da jaridu, da mujallu, a kan matsalolin tsaro.
5. An saurari jawaban shugabannin siyasa, da wakilan tsaro, da malaman addini, masu fashin baƙi, da sarakuna, a kan harkar tsaro.
6. An kuma nazarci wasu sassan adabin baka na waƙoƙi, kamar waƙoƙin tauri da na sata da sauransu.

## 2.0 Wane ne Kassu Zurmi?

Masana irin su Magaji (2016), da Kaura (2017), sun tabbatar da cewa, Makaɗa Alhaji Abubakar Kassu jikan Gandau ne. Shi kuma Gandau mutumen Kurawa ne ta ƙasar Sabon Birnin Gobir. Allah ya yi tafiyarsa wani gari da ake kira Dunfawa, inda a nan ne ya haifi Muhammadu baban Makaɗa Abubakar Kassu. Daga garin Dunfawa sai Gandau, da shi da iyalansa suka koma garin Magarya a ƙasar Zurmi. Bayan wasu shekaru a garin Magarya, sai Muhammadu mahaifin Kassu ya sami gona a garin Kadawa (duk dai a ƙasar Zurmi), sai ya koma can ya bar ƙanensa Abdu Ctito a nan Magarya, a lokacin kuwa har an yi wa Kassu kaciya.[1] Kassu da kansa ya faɗa cewa, asalinsa daga garin Kurawa suke, can ƙasar Sabon Birni Gobir, a wani ɗan waƙa da yake cewa:

Tun da Haliku yay yo ni,
Tun da mai sama yay yo ni,

[1] Kaura, H.L. (2017). Salon Zayyana (Hotancin Zucci) A Cikin Waƙoƙin Kassu Zurmi. Kundin Digiri na Biyu. Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu Danfodiyo, Sokoto.

Ban zo kiɗi ba  Sabon Birni.
To amma in  bancin rashin sani,
Ba baƙo ba ne gida nid dawo
Gida kurawa ba.
(Kassu Zurmi:  Waƙar Alh Sulaiman Sabon Birni)

Laƙabin “Kassu” kuwa, daga sunan “MaiKassuwa” ne, aka taƙaita sunan zuwa “Kassu”, wato wanda aka haifa ranar da kasuwar garin ke ci. Wannan sunan ya fito a cikin wani ɗan waƙarsa:

Yac ce ina hita *MaiKassuwa,*
To amma hwa ba da alheri ba,
Bari ko an hana ni yanzu da rana,
Sai iskan shabiyun dare ya taso,
---  (Kassu Zurmi: Waƙar Nomau Namgarya)

Alhaji Abubakar Kassu ya rayu tsakanin ƙayyukan Kadawa da Magarya, kuma a nan ya girma tare da mahaifinsa. Ya yi Karatun Allo gwargwadon hali. Bincike ya nuna cewa Kassu Zurmi ya yi auren fari, da ya ƙara girma kuma sai ya ci gaba da ƙara mata har sai da ya cika tsinkensa, wato mata huɗu. Allah ya albarkaci Kassu da ‘ya’ya goma sha biyu maza shida mata shida, kuma su ma ‘ya’yan nasa sun hayayyafa suka sama masa jikoki da yawa. Bayan mutuwar Alhaji Kassu, sai ɗansa Umaru Kaho ya gaje shi a sana’ar kiɗa. Bayan rasuwar Umaru Kaho babu wani daga cikin ‘ya’yan Kassu da ya kama sana’ar kiɗa. Kowa ya kama sana’ar da yake ganin ta fi dacewa da shi. Hasali ma, Usman Kassu hanyar makaranta ya kama (Magaji: 1980).

Alhaji Kassu Zurmi Allah ya ba shi hikima da zalaƙa da shahara da kuma karɓuwa a fagen waƙoƙin maza. Duk da yake waƙoƙin na jarumai ne, amma ba jaruman kawai ke sha’awar waƙoƙin ba. A haka har Kassu ya kai ga samun sarautar kiɗan tauri[2]. Haka kuma, manyan mutane irin su Sir Ahmadu Bello da Sarkin Musulmi Abubakar na III da dai sauran manyan mutane a ƙasar Hausa, sun kasance suna begen ganin Kassu Zurmi a fagen wasa.

## 2.1 Gurbin Kassu Zurmi a Makadan Maza

Ya tabbata a waƙoƙin baka na Hausa, masana sun yi wa kowane makaɗi gurbi, wato inda aka san shi. Kassu Zurmi haziƙi ne a fagen kiɗa da waƙa. Ya yi waƙoƙi iri-iri, daban-daban, kama da na tauri, da na noma da na ɓarayi da na fawa da na ‘yan caca da kuma na farauta. Waƙoƙin Kassu da suka fi jan hankali, su ne  waƙoƙin maza na ’yan tauri da na ɓarayi, domin a wannan zamanin da muke ciki, abin da ya fi damun mutane shi ne matsalar tsaro. Saboda haka, samun maza don su yi mana maganin tsaro, shi ne babban burinmu. A cikin waƙoƙin ɓarayi, Kassu yana karantar da mutane da ɗabi’unsu da za a kiyayewa da su. Wannan kuma shi ne gurbin karatun tsaro ga duniya.

Mu dubi inda yake karantar da mu ɗabi’ar ɓarawo idan ya zo sata, yana cewa:

Sai ya ɗago ɗakim mutum sannu,
In kaɗ ɗan hwalka ya dakanta,
Ɗan banza kak ka gane shi,
Wallahi ɓarawo bila’i ne in dare ya yi.
Sai ka koma kwana,
Kuma ya ɗago ɗakin mutum sannu,

[2] Sarkin Zamfaran Zurmi (Sule) ya naɗa shi Sarkin KIɗan Karma.

In kaɗ ɗan hwalka ya saurara.

In ya aza za ka ganewa,
Sai ya dawo dab baya-baya,
Sai ya yi ma wani allo.
Taɓi yaka yi da hannunai ,
Wai ya yi ma kakkaɓin karnai,
Nan ko ba kare ne ba.
"Ina jin Karen wane,
Ga ya nan ɗan nema bakin ɗaki".
A nan ko ba kare ne ba,
Ɗan banza don kak ka gane shi,
Wallahi ɓarawo bila'i ne in dare ya yi.

Rannan yai tahiya tai,
Kuma sai wata rana ya ɗauki sa'akka,
Kuma ya yi ma wani allo,
Sai ya ebo ruwa dag gidan wani,
Ya zaka ya girke ga ƙohwakka,
Ya ciko ƙwaryar ruwa da ruwa ya girke,
Sai ya ɗago ɗakim mutum sannu,
In kaɗ ɗan hwalka ya saurara,
Kuma in kak koma shi koma,
In yad dahwa, kaɗ ɗan motsa, shi dakanta.

Kuma in yaj ji kamaz za ka ganewa,
Sai ya yi ma allo,
Ruwanga yakan motsa da hannu nai,
Wai ya yi sha kamak karnai,
Nan kau ba kare ne ba.
Sai ya motsa da hannunai ruwan,
Kacal-kacal-kacal,
Ke kin aje ƙwaryar ruwa,
"Kin ji karen gidan wane can ɗan nema
yana sha."

Nan kau ba kare ne ba,
Don dai kak ka gane shi ya taho ma,
Wallahi ɓarawo bila'i ne.

Na tambaye ku ku 'yankallo,
Da wanda ak kimtce duy ya kikkimtsa harkatai,
Da wanda ak kwance sharkaf
kwana na alalai tai,
In an zabura wa ka tcerewa?,
Na gidan Mamman abin tsoro,
Dan kusa Iro sai Mame.
(Kassu Zurmi: Waƙar Na gidan Mamman Abin Tsaro
(Ɗankusa Iro)

Haka ma a waƙar Muhmmmadu Na Sani yana cewa:

> Maganin maza ɗan Sanda,
> Mamman ɗan Sale maganin Samnokin maza
> Masu gigin kwana,
> Mata na hwaɗin ana motci,
> Maigida na hwaɗin kusa na,
> "Haba kusan ɗakinga na,
> Kin san ɗakinga da 'yan neman kusa."
>
> Kun jiya masama,
> Wallahi ka mutun yay kwana
> Yana rena motcin kusa,
> Kowar rena su wata zamba na shawatai.
> (Kassu Zurmi: Waƙar Mamman Ɗangeshe)

Haka kuma, kamar yadda muka gani, duk waɗannan waƙe-waƙe da Kassu ya yi, ya yi su ne ba tare da 'yan amshi ba. Magaji (1980).

## 3.0 Tsaro a Gurabun Waƙoƙin Kassu Zurmi

Kalmar "Tsaro" tana da tushen "tsar-" ne, tana ɗaukar tsarin ɗafa ƙeya da ɗafa goshi. Ana cewa "tsaro" ko "tsari" ko "matsara". A ƙamusun Hausa na Jami'ar Bayero, an bayar da ma'anar "tsaro" da cewa, daga "'tsari' ne aka samu 'tsaro'. 'Tsari yana nufin: kariya, musamman ta Allah"[3] Su kuwa masana suna ganin ƙunshiyar kalmar tsaro tana nufin:

> "Samun cikakkiyar lafiyar jiki, da rayuwa, da abin da rayuwa ke farautowa da adanawa don gaba. Idan da lafiya, an ƙoshi, an adana saura don gobe, an toshe kafar ƙyashi da cecekuce da zai haifar da kowace irin tashintashina, in ji Bahaushe".
>
> (Bunza, 2024:12).

Bisa ga wannan ma'ana, ana cewa tsaro yana nufin kiyaye jama'a daga duk wata fitina ko barazanar abokan gaba da rigingimun cikin gida, musamman abin da ya shafi rayuwarsu da lafiyarsu da mutuncinsu da dukiyarsu.

Babu shakka, matsalar tsaro ta yi tsamari a wannan ƙasa tamu, dalilai na talauci da haɗama da rashin dangana da zalunci da rashin kulawar shugabanni, da sauran dalilai, sun sa yau ɗan Nijeriya[4] ba shi da tsaro a duk inda yake. In yana zaune gida cikin iyalinsa ba shi da kwanciyar hankali, in yana hanya zai tafi aiki ko kasuwanci ba shi da kwanciyar hankali, in yana ofis ko wurin sana'arsa ba shi da kwanciyar hankali. In ya zauna a cikin talauci ba shi da kwanciyar hankali, in kuma ya nemi arziki ba shi da kwanciyar hankali.

[3] (Kamusun Hausa, 2006:453)
[4] Musamman Jihar Zamfara inda Makaɗa Kassu ya fito.

Babu yadda za a yi al'umma ta ci gaba matuƙar babu tsaro, tsaro kuwa ba zai samu ba har sai hukumomin da suke da hakkin tabbatar da shi sun yi aikin da ya dace kuma al'umma ta taimaka wa hukuma. A irin wannan taimakon ne Makaɗa Kassu Zurmi ya tashi haiƙan, ya jagoranci taurarinsa suka taimaka wajen samar da tsaro, musamman a Jihar Zamfara a wancan lokacin.

To da Kassu ya fahimci cewa, maza su ke da tsaro, sai ya kasa waƙoƙi kashi biyu: waƙoƙin Sarauta da waƙoƙin maza (ɓarayi). Dalilin da ya sa ya kawo waƙoƙin ɓarayi shi ne , saboda sata tana da kashi 3 ko 4 na tsaro a duniya: Akwai ɓarayi 'yan fashi ko'ina duniya akwai su, akwai ɓarayi 'yan yankan aljihu, akwai ɓarayi 'yan satar mutane, akwai ɓarayi masu satar dukiya. Sannan kuma akwai ɓarayi na fashi da wayo. Wannan kashi 5 da Kassu ya yi wa ɓarayi, ya buɗa wa jama'a ƙofofin tsaro da ta kamata kowa ya san da su. Wannan ya sa Kassu ke ganin matuƙar aka ambaci ɓarawo, to an yi matsayar tsaro duk inda yake. Don in ɗan'adam ba ya da kaya, me yake nema da tsaro? Idan bai da rayuwa me yake so na tsaro? Idan bai da abinci me yake so na tsaro? In ba ya da lafiya gaba ɗaya, me yake so na tsaro? Saboda haka kuma, sai Kassu ya fito da ƙa'idar tsaro da aka fara ta a Afirika tun shekarar 1750, aka fara tunani da matsalar sata. A wannan shekarar ne aka fara kafa zango a Ghana, yau kimanin shekara 270 da kafa wannan zango (Hausawa suka kafa shi), saboda kula da matsalar sata, musamman da daddare. Shi ya sa Kassu ke cewa:

> Ɓarawo bala'i ne in dare ya yi.

Wannan ya nuna asalin tsaro da daddare ake yin sa. Babu ƙasar da ake tsaro da rana ƙiri-ƙiri, ido na ganin ido, wannan yana kowa yana iya tsaron kansa da rana, amma in dare ya yi, dole kowa ya nemi tsaro, shi ya sa  Kassu Zurmi ke faɗakar da mu, mu mai da hankali in dare ya yi.

Cikin tsaro, Kassu ya kawo muna bayani da ya kamata mu kiyaye da shi, cewa idan kana fuskantar wanda ke ɓata tsaro, kai kaɗai, to kada ka yi tsaye ka ce jihadi za ka yi, ka ja da baya, in an kashe ka komai ba a yi. A ɗauki dukiyarka, kada ka tsaya kariyar kanka, Kassu ya ce, kada ka yi, in babu taimakon mutane, ka nemo mutane a taimake ka a kare ka, don haka yake cewa:

> Yara akan ishe mai abu hwalke,
> Sai dai Allah ya kiyaye,
> Amma ka ga mai abu na ja,
> Ka iske mara abu na ja,
> Ka saki mai abu kay ya gama ma.
> (Kassu Zurmi: Waƙar Adamu Dodo)

Ke nan da ɓarawo da mai kaya , Kassu ya ce wa mai abu!,  jaye!, kada a sabatta ka. Wannan ya nuna cikin ƙa'idar tsaro, idan aka rinjaye ka , kada ka bayar da rayuwarka, in ka mutu, tsaro ya ƙare, amma in kana da rai, to komai ana iya yi.

Don haka a bin da Kassu ya tsinkaya tun wajen shekaru da suka kai 75 yanzu  ga nawa nazari, na aikin da kuka ba ni, ya nuna sata ita ce asalin rashin tsaron kasar nan.

Haka kuma Kassu Zurmi ya nuna mana fatarar abinci da abin sha da ƙarewar su gaba ɗaya, yana saka ƙasa da mutanenta cikin rashin tsaro. Ma'ana, idan tsiya ta yi yawa tana wargaza kowane irin tsaro na al'umma. Wanda ba ya da, babu wurin da yake shakkar faɗawa. Kissar Nomau na Magarya ta ishe mu ishara, inda yake cewa:

Yac ce Kassu ana biɗak ka da doki
Ga ka kana alhwarma.
Nic ce ɗankarma ba ni ƙamnaƙ ƙarya
Wa ka sai mani doki Magarya
Nomau ne ko abin tuwo ba ya da shi
Sai yac ce ai da tarbace za a saye
Da tarbace za a saye
Su wa su wa sun ka shiga?
Na san dattiɓan Magarya zana mani su
Cikinsu na san kowa
Na san mai iya yi
Yac ce masalin Saraki ya ce a saye
Gardaye Sanda ya ce a saye
Sarkin hwawa Abdu ya ce a saye
(Kassu Zurmi: Waƙar Nomau)

Haka kuma Kassu ya nuna mana muhimmacin aure a wajen samar da tsaro a duniya. Shi ya sa kowace ƙasa duniya ana yin aure, don shi ke tabbatar da samun tsaro a kowane gida. Idan babu aure babu tsaro. Kassu ya faɗakar da mu ƙissar Shaya ɗan gidan Labbo, cewa gidansa ba ya da tsaro don bai iya ajiye mata.

Labarin Shayi ɗan gidan Labbo.
'yammata sun walwale baikonsu,
Sun ce Sha-yaya za shi rankonsu.
Shi muka so ka ba mu labari in akwai gidan kirki.
Nic ce yau kam dattijo kun ɗamarshe ni.
Ya hi ku koma ku sake ɗan sheda
Na'abu ɗan 'uwana ne,
Mutun kau bai shedaɗ ɗa 'uwanshi ko hwada.
Kassu amana Allah ka ba mu labarai
Ni kau amana Allag ga ɗai ka sha man kai.
In nab bi amana Allag ga na yi ɓatanci.
Amma hwa ku ba shi in kuna ba shi,
Na'abu dai ɗa ne.
Ba haka munka so ba ɗan yaro,
Ai mun san ɗa ne tun da anka haihe shi.
Ba mu labari in akwai gidan kirki.
Nic ce i gaskiyakku dattijo.
Mutum ba za ya kai ɗiya tai ba gidan da ba abin kirki.
Amma hwa ku ba shi in kuna ba shi ,
Sai ɗiyad dattiɓai kaɗai ka amren Sha-yaya
Ɗan gidan Labbo, Na'abu
Tunda kowa amre shi ita ka cishe shi.
Ta biya kuɗɗin garin Karen kyamsu.
Sannan ta yi mai abin ruhwa koren .
Kana ta koma yin dabbalin abin ɗamri.
Dattijo yat tashi .
Yab buge riga yay yi cikin zaure.
Yac ce ma ɗiyatai ga tciyakki nan samna,

ke da kinka zaɓo shi.
(Kassu Zurmi: Waƙar Shayi)

### 3.1 Nau'o'in Matsara

A cikin kowace ƙasa, akan samu matsara waɗanda amanar tafiyar da ingantaccen tsaro yana hannunsu. Idan sun tsare aikinsu, al'umma za ta samu tsaro. Idan kuwa suka yi sakaci da aikinsu, to al'umma ta shiga uku. Daga cikin nau'o'in matsara akwai:

#### 3.1.1 Kai

Daga cikin nau'o'in matsara akwai tsaron kai. Wato mutum ya kula da kansa. Ya iya samar wa kansa kariya ta hanyar ƙarfin tuwo, a yi gaba da gaba, mutum ya ƙwaci kansa. Ko kuma ta hanyar neman magungunnan kare kai da jikinsa. Kassu ya bayar da shawara cewa, idan dai har ɓarawo ya mame ka, kuma kai kaɗai ne, yi ƙoƙari ka nemi mafita na rabuwa da shi. Har in ta kai ga ka haƙura ka sakar masa kayan ya fi. Inda yake cewa:

Yara akan ishe mai abu hwalke,
Sai dai Allah ya kiyaye,
Amma ka ga mai abu na ja,
Ka iske mara abu na ja,
Ka saki mai abu kay ya gama ma.
(Kassu Zurmi: Waƙar Adamu Dodo)

A nan, Kassu yana bai wa mai kaya shawara cewa ya guji yin gaba da gaba da ɓarawo.

#### 3.1.2 'Yandoka

'Yandoka su ne nau'o'in mutane waɗanda ke taimakawa wajen samar da tsaro cikin al'umma. A gargajiyance, akwai dogarai waɗanda samar tsaro yana a kansu. Bunza, (2014:429) ya kawo jerin matsara na gargajiya kamar haka:

a) Zagi: Mai shiga gaban sarki in ana tafiya.
b) Yari: Mai kula da kurkuku
c) Hauni: Mai zartar da hukuncin kisa.
d) Majasirdi: Mai yi wa dokin sarki sirdi
e) Kat-ta-kwana: Mai kai sanarwar yaƙi.
f) Mazawaje: Mai busa kugen yaƙi.
g) Lihidda: Mai kula da matattu da accakwamar yaƙi (wanɗanda aka yi wa mummunan rauni).
h) Sarkin Karma: Shugaban dakarun ƙasa ('yantauri) masu gora.

Waɗannan su ne masu muƙaman tsaro a cikin al'umma a gargajiyance. Da zamani ya zo sai aka maye su da 'yansanda. Kassu ya tuhumi 'yansanda wajen haɗe baki da ɓarayi. Wanda duk aka ba tsaron kaya ya sace su, ya fi ɓarawo laifi da ban takaici. Idan ɗandoka ya karya doka ya ce wa sauran jama'a kowa ya je ya karya ta ke nan. Don haka Kassu Zurmi ya nuna wani ɓarawo ya saba da 'yansanda, saboda haka ba ya jin fargaba a wajen satarsa. Yana cewa:

Ya dai saba da 'yandoka,
Ya dai saba da 'yandoka,
Yanzu ha alƙali ba ya nuni nai,
Sai dai ya yi mai jawabi,
In yas saɓa mai ya saɓa mai.

A nan, Kassu ya nuna wannan ɓarawo ya saba da ‘yan doka da alƙalai masu kama ɓarayi da hukunta su.

Daga cikin taurarin Kassu ‘yan tauri su ke sahun gaba wajen samar da tsaro a ƙasar Hausa. Da babu ‘yan tauri cikin garuruwanmu da tsaro ya shiga uku. Shi ya sa a ƙasar Gobir da Zamfara, lokacin da akwai ‘yan tauri “na ƙwarai”, babu tashitashina a wannan yanki. Duk abin da ya kawo taɓarɓarewar tsaro a yanzu shi ne babu ‘yan tauri, ’yan kaɗan ne suka rage a yanzu. Duk sauran je-ka-na-yi-ka ne. Waɗannan ‘yan kaɗan ɗin, su ne suke yin banga ko sa-kai a yanzu a waɗannan yankuna na Gobir da Zamfara. Duk da yake dai ckinsu ɗin ma akwai ɓara-gurbi masu haɗa kai da ’yan ta’adda, suna lalata dokokin tsaro.

### 3.1.3 Makamai

Makamai suna taka rawa sosai wajen samar da tsaro. Su ne ma kan gaba a cikin samar da tsaro. Da makami ake yi wa jama’a barazana, musmman waɗanda suke son kare lagon tsaro. Haka su ma masu ɓarnar, da makami ne suke yin barazanar tayar da zaune tsaye. Makaman yaƙi iri-iri ne. Akwai na gargajiya akwai kuma na zamani. Daga cikin na zamani akwai bindiga da bam da borkonon tsuhuwa da rigar sulke da kyamarori da jiragen yaƙi da makaman harbo jirgin sama da sauransu. A gargajiyance kuwa, akwai makaman yaƙi da suka haɗa: sanda da takobi da adda da gatari da wuƙa da mashi da sauransu. Kassu yana cewa:

Kuma sai ya ɗago ɗakin mutum sannu,
Kwana ɓarawo ne in yash share ka shi ke nan,
Sai ya ga *takobi* ya janyikke,
Shi yi wuri ya iza ma yaro nai, shi dawo,
Akwai wata *‘yag gitta* ya ɗaukikke,
Shi yi wuri ya iza ma yaro nai shi dawo,
Iro sai mame na gidam Mamman abin tsoro.

### 3.1.4 Magani

A cikin waƙoƙin Alhaji Abubakar Kassu Zurmi, akwai abubuwa da dama dangane da magungunan kare kai/jiki, waɗanda taurarinsa ke amfani da su. Saboda haka, tauri ko sata ko farauta, ba su yiyuwa sai da magani. Kassu yana cewa:

Ashe Musa ya ci magani
Bai samu wurin gwaji nai ba,
Suna ta bugu suna sara
Dud dai ba a huda kai nai ba.
Ku am manyan hwaɗa
Musa na ƙasad Ɗan’Ali mai tauri.
...
Nace ce “ko ba ka ji tsoho,
Hillani sun sabatta ka
Yac ce “Ɗan’Ali koma gida,
Ja dan nan ba ni son ƙarya
Ba kau yaƙin takobi ba,
Don su Musa na tahowa gida”
Manyan hwaɗa

(Kassu Zurmi: Waƙar Musa na ƙasaɗ Ɗan'Ali wan ƙarhi).

A nan, Kassu yana son ya nuna Tsoho ya shirya yaransa, saboda haka bai da fargaba, don an ce masa sun haɗu da hillani (Fulani).

Haka kuma, Kassu ya wayar muna da kai cewa, magungunan wasu ba shan su ake yi ba, sai dai a rataya a jiki, kamar su kambu da dagumi da laya, da guru/karhu da ɗamara da sauransu. Yana cewa:

Ba a ma kau-da-bara,

Wani ya gwada baduhun bai ɓace ba.

---

Kau- da-bara wata laya ce idan mutum yana tare da ita a jikinsa, duk abin da aka jefe shi da shi sai ya kauce, bai faɗawa a jikinsa, balle ya illata shi. Ita kuwa layar baduhu ita ce wadda ake ɓacewa, kuma a ci gaba da tafiya a ɓace, ba a ganin mutum.

Har ila yau, Kassu ya sanar da mu wuraren da akan sami waɗannan magungunan, wato wuraren mallammai da kuma sauwoyi da saƙesaƙi na itace. Kamar inda yake cewa:

Tauri wuya garai sai a yi ƙoƙari,
A sha mallammai a ɗebi sayyu a yi kariya,
In an ƙiya ana cim ma sanin wani.
(Kassu Zurmi: Waƙar Shehu Ɓuraguji)

Haka kuma akwai inda yake zuga Nomau yana cewa:
Sai ga Nomau ana ta gyaran layu,
Da kambuna za a hwashe.
(Kassu Zurmi: Waƙar Nomau)

Da wannan muke jaddada cewa dai tauri ba tsafi ba ne, a daure a sha a yi wanka kuma a ɗaura, domin kariyar kai da kaya.

### 3.1.5 Waƙa da Kiɗa

Waƙa da kiɗa ko kirari ko take, da su ake tayar da jarumtakar mazaje. A zamance, kowace ƙasa tana da take, wanda ake yi wa 'yan ƙasar don a zuga su a wajen yaƙi ko a wajen ƙwallo, ko don a saka musu kishin ƙasarsu. A gargajiyance ma abin haka yake. Akan yi wa jarumai waƙa ko kirari ko a kiɗa takensu, nan da nan sai jaruntaka ta motsa, a yi abin da ake son yi. In gyara in ɓarna. Kassu Zurmi ya fito da wannan nau'in na kiɗa da waƙa don samar da tsaro, ta hanyar motsa zukatan jarumansa, yana cewa:

Mai Babarbara Shehu Ɓuraguji,
A'a tun da kuna ɓurkutar kalangai,
Ku naɗe wuta, ku kashe wuta.

Kuna wha jin kiɗin tad da hayaniya,
Mai Babarbara Shehu jiran gado,
Banawa ko ba ku jin kalangan kariyar wuƙa?

Kuna hwa jin batutuwan tad da hayaniya.

Ban san kai ne Namusa,
Babu ruwan Kassu tun da ba ni ka gama ku ba,
Amma hwa ina gida ina ba ku zuga-zugi,
Kun ji kalanguna suna hwadin wani ya kashe wani,
(Kassu Zurmi: Waƙar Shehu Ɓuraguji)

A nan Kassu Zurmi ya nuna yana zuga su ne da kalangai, don jaruntaka ta motsa.

### 3.1.6 Kyauta

Kyauta a nan, ana nufin bayar da wani abu ko wata dukiya ga wanda ya nuna bajinta ko jarumtaka, don ƙarfafawa, yana ƙara musu ƙarfin guiwa. Kamar yadda ake ƙara wa sojoji da sauran masu kayan sarki lambar girma ko ta yabo, idan suka dawo daga yaƙi kuma suka samu nasara. Haka yake ko a gargajiyance. Sarki kan yi wa jarummai kyauta ta musamman don ƙarfafa su wajen samar da tsaro. Shi ya sa Kassu ya nemi doki ga Noamu, don ya san ba ya da shi, amma ya ba shi shawara ya nema ga saraki, in kuma an ƙiya, ya bi mugunyar hanya, wadda za ta sa dole a ba shi dokin. Yana cewa:

Doki da gangami sai Nomau na Magarya,
Uban Balindo shi ya ishe ni hak Kadawa,
Yac ce Kassu ana biɗak ka da doki,
Ga ka kana alhwarma,
Yac ce Dankarma ba ni ƙamnak ƙarya,
Wa ka sai mani doki Magarya?
Nomau ne ko abin tuwo ba ya da shi.

Yac ce da tarbace za a saye,
Da tarbace na san kowa Magarya,
Zana man su, su wa suwa suk ka shiga,
Yac ce masalan Saraki yac ce a saye,
Gardaye Sanda ya ce a saye,
Ɗanmani Magaji yac ce a saye,
Kuma Labo Sarkin Maƙera yac ce a saye,
Sarkin fawa Audu yac ce a saye.
(Kassu Zurmi, Waƙar Nomau).

Wannan faɗakarwa ce Kassu yake yi zuwa ga shugabanni, na su riƙa yin kyauta ga jarummansu, don inganta tsaro.

### 4.0 Sakamakon Bincike

Wannan bincike ya gano abubuwa da dama a cikin waƙokin Kassu Zurmi da suka shafi tsaro da ta'addanci. Daga cikinsu akwai:

1. Akwai faɗakarwa dangane da yadda ɓarayi ke yin sata musamman da dare.
2. Haka kuma, Kassu ya nuna nasiha ga "mai abu", wato mai dukiya , wanda ɓarawo ya kai hari a gidansa, kuma babu kowa mai kama masa, to kada ya ja da ɓarawo, don gudun salwantar rayuwarsa, ko wani sashe na jikinsa.

3. Kassu ya nuna mana cewa tsaro bai samuwa da fatara ko rashin abinci ko abin sha. Ba shi yiyuwa irin ƙasar Nijeriya da aka yi zanga-zanga a kan yunwa, kuma a ce a samu ingantaccen tsaro.
4. Haka kuma, waƙoƙin Kassu sun fito da illar rashin iyali/mata a gida a wajen samar da tsaro.
5. Aikin ya gano cewa bai kamata ba mai dokar barci ya kama gyangyaɗi. Saboda yadda 'yandoka suke yi da masu laifi, da ci da ceto, yana hana samar da ingantaccen tsaro a cikin ƙasa.
6. Aikin ya gano cewa, rashin tsaron da ake samu a yankin Zamfara da Gobir, bai rasa nasaba da rashin ingantattun 'yantauri irin waɗanda suka yayi da Kassu Zurmi.
7. A ƙarshe, aikin ya gano cewa tauri ba tsafi ba ne. Kuma akwai bukatar jama'a su ci, su sha kuma su ɗaura, domin kariyar kai da kaya.

## 5.0 Kammalawa

Kamar yadda bayani ya gabata tun a taken wannan maƙala cewa, kowace irin al'umma ta duniya, tsaro shi ke kafa ta. Babu yadda za a yi al'umma ta ci gaba matuƙar babu tsaro. Tsaro kuwa ba zai samu ba har sai hukumomin da suke da haƙƙin tabbatar da shi sun yi aikin da ya dace kuma al'umma ta taimaka wa hukuma. Idan aka nazarci waƙoƙin Kassu Zurmi sun fito da hanyoyin da ya kamata a bi, don a samu ingantaccen tsaro a cikin al'umma. Wajibi ne matsara su tabbatar da sun bi shawarwarin Kassu Zurmi, domin samar da ingantaccen tsaro a cikin ƙasa, musamman yankin Zamfara da Gobir, inda shi Kassu ya fito.

**Manazarata**


Bunza, A.M. (2014). *In Baka san Gari ba Saurari Daka: Muryar Nazari Cikin Tafashen Gambo.* Cairo: Elkods Printing House.

Funtua, A.I. (2015). "Nazari a Kan Waƙoƙin Makaɗan Baka na Hausa a Jihar Katsina Daga 1978 Zuwa 2012". Kundin Digiri na Uku (Ph.D Thesis). Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya. Kano: Jami'ar Bayero.

Gusau, S.M. (1988). "Waƙoƙin Makaɗan fada: Sigoginsu da Yanaye-yanayensu". Kundin Digiri na uku (PhD Thesis). Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya. Kano: Jami'ar Bayero.

Gusau, S.M. (2003). *Jagoran Nazarin Waƙar Baka.* Kano: Benchmark Publishers Limited.

Gusau, S.M. (2008). *Waƙoƙin Baka a Kasar Hausa: Yanaye-yanayensu da Sigoginsu.* Kano:Benchmark Publishers Limited.

Gusau, S.M. (2009). *Diwanin Waƙoƙin Baka: Zaɓaɓɓun Matanoni na Waƙoƙin Baka na Hausa.* Kano: Century Research and Publishing Limited.

Gusau, S.M (2014). *Waƙar Baka Bahaushiya (The Hausa oral song)*. Kano:Professional Inaugural Lecture, Series NO.14. Jami'ar Bayero.

Kaura, H.L. (2017). "Salon Zayyana (Hotancin Zucci) A Cikin Waƙoƙin Kassu Zurmi". Kundin Digiri na Biyu. Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya. Sokoto: Jami'ar Usmanu Danfodiyo, Sokoto.

Magaji, A. (2016). *Kassu Zurmi da Waƙoƙinsa*. Ibadan: Specrum Books Limited.

Satatima, I.G. (2009). "Waƙoƙi Baka na Ɗarsashin Zuciya: Yanaye-yanayensu da Sigoginsu". Kundin Digiri na uku (PhD Thesis). Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya. Kano: Jami'ar Bayero.

Sulaiman, I.I. (1983). “Waƙoƙin Ɓarayi”. Kundin Digiri na uku. Sashen Harsunan Afirka da Al’adu. Zaria: Jami’ar Ahmadu Bello.

Usman, H.S. (2011). “Tarihi da Waƙoƙin Makaɗa Abubakar Kassu Zurmi”. In *Funtuwa, A.I. da Gusau, S.M. (Editoci) Waƙoƙin Baka na Hausa.* Kano: Century Research and Publishing Limited.

Yahya, A.B. (1997). *Jigon Nazarin Waƙa*. Kaduna: FISBAS Media Services.

Yahya, A.B. (2001). *Salo Asirin Waƙa.* Kaduna: FISBAS Media Services.